


*CIBIYAR BUNKASA FASAHAR SADARWA DA CIGABAN AL'UMMA (CITAD) NA BAYAR DA HORO KAN ILIMIN NA'URA MAI KWAKWALWA*

# MUJALLAR CITAD RADIO
## RADIYON DA ZAKU SAURARA
www.citad.org/radio

Volume 2, issue 2


**19-01-1443 AH**
**27-08-2021 AD**

## LABARAN CIKI

| | |
|---|---|
| **Muryar Matasa** | 1 |
| **Watch Dog** | 2 |
| **Ilimin 'Ya Mace** | 3 |
| Sharhin Yau da Kullum | 4 |
| **Shiri Na Mussamman** | 5 |
| **Siyasa Da Rayuwa** | 6 |
| **Ilimi Da Matasa** | 7 |

**Zaku iya sauraro da sauke manhajar CITAD RADIO ta wannan likau din dake kasa**



*https://play.google.com/store/apps/details?id=com.citad.org&hl=en&gl=US*

# CITAD, NOA, Da Arewa Rediyo Za Su Yi Haɗin Gwiwa Wajen Yaƙi Da Cin Zarafin Mata

Hukumar wayar da kan al'umma ta ƙasa NOA da cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa da Cigaban Al'umma, CITAD, sun sha alwashin yin haɗin gwiwa wajen yin aiki tare akan yaƙi da cin zarafin mata da ƙananan yara a jihar Kano.

Babban daraktan Hukumar ta NOA reshen jihar Kano, Malam Lawan Shuaib Makarfi ne ya tabbatar da hakan a lokacin da jami'an cibiyar ta CITAD su ka kai masa wata ziyara a ofishinsa da ke Kano.

Malam Lawan Makarfi ya ce hukumar ta NOA tana da dakarun sa kai guda goma (10) a kowacce mazaba da ke jihar Kano. A dan haka za su yi amfani da su wajen wayar da kan al'umma akan wannan mummunar ɗabi'ar nan ta cin zarafin mata.

Ya ce yaƙi da cin zarafin mata da ƙananan yara abu ne da rataya a wuyan kowa. A dan haka akwai bukatar al'umma ta tashe tsaye wajen yaƙi da masu aikata wannan dabi'a.

A nata ɓangaren jami'a a ɓangaren fasaha kuma shugabar gangamin yaƙi da cin zarafin mata ta cibiyar CITAD din Zainab Aminu, ta bayyana cewa la'akari da irin yadda ake samun ƙaruwar cin zarafin mata da ƙananan yara a jihar Kano, wanda hakan ke jefa iyaye cikin halin rashin tabbas ya sanya cibiyar ta fara wannan gangami wanda ya samu tallafin gidauniyar Ford da ke ƙasar Amurka.

Zainab Aminu ta ce tuni cibiyar ta CITAD ta himmatu wajen baiwa wakilanta na sa kai da ke makarantun gaba da Sakandare horo na musamman akan yadda za su dinga ba ta bayani akan faruwar wannan al'amari ta hanyar amfani da wata manhaja da ake sakawa a wayoyin zamani na tafi - da - gidanka.

Haka kuma ta ƙara da cewa cibiyar ta CITAD za ta yi haɗin gwiwa da hukumar kare hakkin bil'adama ta ƙasa da kuma rundunar ƴan sanda da hukumar Hisba da kungiyoyin fararen hula domin yaƙi da wannan mummunar ɗabi'ar. ya zama ruwan dare a sassan Najeriya.

Haka kuma wata kididiga da hukumar da ke kula da ƙananan yara ta Majalisar Ɗinkin Duniya ta nuna ana cin zarafin yaro ɗaya a cikin kowane uku a Najeriya, ya Allah ta hanyar fyade ko wani nau'in cin zarafin na daban.

# CITAD, NOA, Da Arewa Rediyo Za Su Yi Haɗin Gwiwa Wajen Yaƙi Da Cin Zarafin Mata - cont

A nata ɓangaren jami'a a ɓangaren fasaha kuma shugabar gangamin yaƙi da cin zarafin mata ta cibiyar CITAD din Zainab Aminu, ta bayyana cewa la'akari da irin yadda ake samun ƙaruwar cin zarafin mata da ƙananan yara a jihar Kano, wanda hakan ke jefa iyaye cikin halin rashin tabbas ya sanya cibiyar ta fara wannan gangami wanda ya samu tallafin gidauniyar Ford da ke ƙasar Amurka.

Zainab Aminu ta ce tuni cibiyar ta CITAD ta himmatu wajen baiwa wakilanta na sa kai da ke makarantun gaba da Sakandare horo na musamman akan yadda za su dinga ba ta bayani akan faruwar wannan al'amari ta hanyar amfani da wata manhaja da ake sakawa a wayoyin zamani na tafi - da - gidanka.

Haka kuma ta ƙara da cewa cibiyar ta CITAD za ta yi haɗin gwiwa da hukumar kare hakkin bil'adama ta ƙasa da kuma rundunar ƴan sanda da hukumar Hisba da kungiyoyin fararen hula domin yaƙi da wannan mummunar ɗabi'ar.

A wani cigaban shugaban gidan rediyon Arewa da ke jihar Kano Malam Shehu Bala Kabara ne ya bayyana cewa tashar ta su a shirye ta ke wajen baiwa cibiyar CITAD goyon bayan akan gangamin da ta ke yi na yaki da masu cin zarafin mata da ƙananan yara.

Malam Shehu Bala Kabara, wanda ya samu wakilcin Widad Isma'il da Nura Haruna Mudi, ya bayyana hakan ne a lokacin da su ke karɓar bakuncin jami'an cibiyar bunƙasa fasahar sadarwa da cigaban al'umma CITAD a ofishinsa.

Ya ce gidan rediyon Arewa zai yi amfani da shirye-shirye sa wajen wayar da kan al'umma akan illolin da ke tattare da cin zarafin mata da ƙananan yara.

Hakazalika ya ce hukumar gidan rediyon za ta duba yadda za ta baiwa cibiyar ta CITAD wani fili kyauta da za ta

**CITAD Ta Ba Da Gudummawar Kwamfuta ga Kungiyar Raya Matasan Jihar Gombe Mai suna AZAMA**

A yau 23 ga Agusta na wannan shekarar da muke ciki, tawagar Cibiyar bisa ga jagorancin Kwamared Yakubu Ali sun kai ziyarar tuntuɓa ga C I T A D . Manufar ziyarar dai ita ce don hada hannu tare jinjinawa CITAD kan dimbin aiyukan da ta ke wanda ya shafi rayuwar al'umma a Najeriya.

Da yake jawabi a wajen taron, Kwamared Yakubu ya ambaci wasu daga cikin dalilan da suka kawo ziyarar sune: Hadin gwiwa a fannin horon Matasa da Mata kan harkokin kasuwanci da kumq bayar da horo.

Tun da farko, sakataren kungiyar, Kwamared Sadiq Yahya ya bayyana cewa kungiyar ta shafe shekaru uku tana gabatar da aiyuka kan yaki da talauci, rashin aikin yi da jahilci ta hanyar horar da matasa dabaru daban -daban, ilimi, da kuma karfafa gwuiwa.A nasa jawabin, Babban Daraktan CITAD, Injiniya Yunusa Ya'u ya godewa tawagar bisa ziyarar da ta kawo wa CITAD tun daga jihar Gombe.

Ya ci gaba da ba su shawara kan jajircewa da zama masu juriya, da aiki tukuru, da yin hakuri da sanya fifikon al'umma a gaba a kan duk abin da suke yi. Ya kuma ba su tabbacin cewa kofar CITAD koyaushe a bude take don taimako, da bada shawarwari. A ƙarshe ya gabatar da kyautar kwamfutoci bakwai (7) ga



WWW.CITAD.ORG/ RADIO

Main Office:3rd Floor, NSITF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 080-68078282
080-54362931
070-33427467
E-mail: info@citad.org,
Website: www.citad.org

www.citad.org

**Center For Information Technology and Development**

**BABBAN EDITA**
Hamza Ibrahim

**EDITA**
Buhari Abba Rano

**MATAIMAKIN EDITA:**
Gazzzali Haruna

**MAI KULA DA TSARE-TSAREi:**
Ali Sabo

**Mai Kula Da Dab'i**
Salim Sani Shehu

#Kansis

Ko kun san cewa a shekarar 2019 fiye da 500 ne daga ciki da wajen Najeriya su ka halarci gangamin taron masu amfani da shafukan sadarwa mai lakabin KANSIS2019, wanda cibiyar bunƙasa fasahar sadarwa da cigaban al'umma CITAD ta ɗauki nauyi?

A wannan karon cibiyar ta CITAD ta fara yin rijistar irin wannan mashahurin taro a karo na biyu, wanda zai gudana a cikin watan Oktoba. Kuma tuni shahararrun masana daga ɓangarori daban-daban sun shirya tsaf domin gabatar da ƙasidu tare da lakcoci akan abubuwan da su ka shafi tabbatar da adalci da wayar da kan al'umma da sana'o'in dogaro da kai da ma yadda ya kamata ku yi amfani da shafukan sadarwar zamanin bisa ƙa'ida!

Domin ƙarin bayani maza ku garzaya ƙasan wannan rubutun dan yin rijista.

